## ALLAH YA BAYYANA KANSA TA WURIN YESU - Babi na 1 - 7

A cikin wannan shekara za mu dubi sashi na wasiƙar Bulus zuwa ikilisiyar Kiristi a Roma. Damuwarsa a lokacin shi ne saɓanin Yahudawa da suka tuba sun tayar game da sharuɗan ceto. Ainihin batun shi ne adalci ta wurin bangaskiya amma a cikin wasiƙar Bulus ya tattauna dukan muhimman batu na bangaskiyar Kirista.

Ko da yake yanayinmu a yau zai iya kasancewa dabam, bayyanin tattaunawar Bulus zai iya taimakon mu ga damuwar addini na son kai da kuma mutane da ke son dogara ga abubuwa kamar zama memban ikilisiya, baptisma ko baye baye na ruhu a matsayin hanyar ceto.

# Babi na 1 — Labari mai Daɗi!

### Romawa 1:1-17

GABATARWA MINTI 5

**MANUFA:** Domin mu sami ƙarfin halin gabatar da kanmu ga waɗansu a matsayin Kirista kirayayyu na Allah.

Ikilisiya ta Roma ta yi ƙarfi tana kuma girma; kowa yana zancen yadda addinin Kirista ya yaɗu a wannan babban birnin jihar.

Bulus bai taɓa saduwa da Kirista na Roma ba, saboda haka ya ɗauki zarafi a farkon wasiƙarsa don ya gabatar da kansa garesu. Yana so ya kafa dangantaka mai kyau da su don ya buɗe hanya domin ainihin batun. Ya sami labarinsu, yana yi masu addu'a kullayaumi kuma yana da marmarin ya ziyarce su.

Ya furta masu cewa ba wai yana zuwa da wani sabon labari kamar yadda waɗansu ke shawarta ba. Shi ne wannan bishara wanda Allah ya yi alkawarinsa tun a tsohon alkawari. Yana so su sani cewa lalle jawabin bishara na Kirista ba tarin dokoki da ka'idodi ba ne amma "albishiri na farin ciki mai yawa" (Luka 2 v.10).

TAMBAYOYIN TATTAUNAWA MINTI 30

**Karanta Romawa 1:1-7**

**Gabatarwa da gaisuwa:**

1. Menene ma'anar waɗannan hanyoyi uku da Bulus ya kwatanta kansa (aya 1)?

2. Waɗanne muhimman abubuwa guda uku Bulus ya yi game da yanayin jawabin bishara (aya 1b-4)?

   Bayyana dalilin da ya sa kowanne yana da muhimmanci yau kamar yadda da yake ga Kirista na Roma.

3. Bulus ya tabbata Allah ne ya kira shi ga aikin bishara na Yesu Kristi (aya 5).

   Ta Yaya yake ƙarfafa bangaskiyar waɗannan masu bi (aya 6-7)?

**Karanta Romawa 1:8-17**

**Zuciyar shaida bishara:**

4. Yaya kake ji waɗannan masu bi za su sami ƙarfafawa daga damuwa da ƙaunar da Bulus yake da shi gare su da niyarsa ya ziyarce su (aya 8-13)?

## CI GABA DA TAMBAYOYI

5. Menene ya hana shi yin wannan ziyara har zuwa yanzu (aya 10)?

   Ba da misali na yadda nufin Allah yakan zama abu mai sa ka marmari ga:
   a) addu'arka da
   b) ayyukanka

6. Yaya Bulus ya bayanna dalilin niyarsa na yaɗa labari mai daɗi na saƙon bishara (aya 16-17)?

## TAKAICIN KOYARWA MINTI 5

Bulus muhimmin shugaba ne na ikilisiya, amma yana kulawa kwarai da sauran membobin ikilisiya. Yana so waɗannan masu bi su sani yana addu'a kullayaumi domin su kuma yana marmari ya ziyarce su.

Wannan ziyara yana da muhimmanci gare shi, ba domin kwaɗayin arziki ko don ya yi wa'azi a babban birnin jiha ba. Ya so wannan dama ya zama hanyar albarka da ƙarfafawa ga ikilisiya da kuma yaɗa bishara ga mutanen birni. Kamar da yawa daga cikin sanannun shugabannin ikilisiya da suka sami albarka ta wurin bangaskiyar membobi, Bulus ma bai yi girman kai ba, ya gane cewa shi ma zai sami ƙarfafawa daga wannan ziyara da zai kai wa ikilisiyar Roma.

Har yanzu Allah bai bari wannan ziyara ya yiwu ba, amma Bulus ya ci gaba da yin addu'a cewa ya yiwu a lokacin da Allah ya ga ya yi daidai kuma a nashi tafarki. Ya kamata wannan ya zama abin bishewa a cikin dukan ayyukanmu da addu'o'inmu.

ya ba shi, ba don ya yi alfahari da shi ba, amma abin muhimmi gareshi da ya kamata ya faɗa wa sauran mutane. Tana da ikon ceton da canja rayuwa ba ga masu hikima kaɗai kamar yadda Girkawa suka bada gaskiya ba, ko kuma ga mutane masu addini kawai kamar yadda Yahudawa suke tunani ba amma ga kowane mutum da ya karɓi saƙon Allah.

Yana da muhimmanci mu kama wani abu daga so na kwarai da Bulus ke da shi wa saƙon ceto, don ya zama mana wajibi mu gaya wa waansu game da shi.

## AYYUKAN YI MINTI 20

Ku rabu cikin ƙungiyoyin mutum huɗu ko biyar, ku tattauna, ku yi addu'a tare.

1. Ka bayana yadda wani lokacin da kake tare da wasu mutane har suka yi mamaki da suke ji kai ne Kirista.
   Menene sakamako a lokacin domin
   a) kanka? b) ƙungiyar mutane?

2. Kowane mutum ya faɗi yadda zai bayyana bishara ga wanda bai taɓa zo sujada ba. Ka nemi hanyar gaya wa a kalla mutum ɗaya wannan sati.

Karanta **Romawa 1:18-32** cikin makon nan.

**Raira waƙa:** "Yesu dutsen cetona..."

**ADDU'A**

* Gode wa Allah domin abin mamaki na kyautar ceto cikin Almasihu.
* Yi addu'a domin taimako don sake samun murna na cetonka da kuma marmarin yaɗa shi.

**HADDACEWA:** Romawa 1:16